# Wa Kake So Ka Zama?

Mahalarta taron za su bincika halayyarsu a intanet da abubuwan da suka ƙirƙira kuma suka raba waɗanda suka danganci manufarsu (misali., abubuwan da suka danganci ci gaban rayuwa, karatu, abubuwan da suke so su cimma a rayuwa). Za su bincika yanda za a kula da halayya a intanet wadda aka yi la’akari da ita a matsayin darasi, dandali, suna, abubuwan da ke wakiltar kai, da saitunan sirri.

## Kayayyaki darasi

Takardar Darasi a kan Halayyata a Intanet

# Halayyata a Intanet

## Tattaunawa

### Sanar da Ɗalibanka

Bari mu ɗauki minti ɗaya domin mu yi tunani a kan yanda muke yin hulɗa da mutane daban-daban dangane da yanda su ke. Za ka iya nuna halayya daban a gaban abokanka a kan yanda kake nunawa a gaban iyalinka ko malamanka a makaranta. Haka kuma za ka iya nuna halayayya mabambanta a wurin ko a lokacin — ta hanya guda tare da abokai a makarantarka, sannan ta wata hanyar daban kuma tare da waɗannan abokan dai a lokacin da kuke tare bayan an tashi daga makaranta.

### Sanar da Ɗalibanka

Dukkanmu mutane ne da za mu ɗan iya bambanta dangane da inda muka fito da kuma waɗanda muke tare da su. Kana da makamaciyar damar da za kula da abubuwanka da kuma kai kanka a kan yanda za ku bayyana ga jama'a ta intanet, kuma zai iya taimakawa a fara yin tunani game da yanda kake so wasu mutanen su kalle ka a intanet.

Fitattun mutane (misali., waɗanda ke masana'antar kiɗa da / ko fim [fina-finai / TV], fitattun 'yan siyasa, shugabannin 'yan kasuwa) suna yin wannan a kowane lokaci. Ka yi hankali wajen shirya kowane ɓangare na nau'in kayansu da kasancewa a bainar jama'a, daga abubuwa a dandalin sadarwar zamani (misali., hotuna, bidiyoyi, aike masu ɗauke da rubutu) don yin intabiyu, suna yin ƙoƙari domin su ɗaukaka su ga masoya da yawa ko abokan ciniki.

Ba lallai sai ka zama wani fitaccen mutum wanda ke da biliyoyin-daloli a dabarun kasuwancin ba. Amma yana da muhimmancin ka yi tunani a kan wanda zai iya ganin kasancewarka a intanet sannan ka tsara yanda za ka bayyana a intanet a gaba.

## Yin hulɗa

### Tattaunawa a Aji

Shirya maharta taron bibbiyu.

### Tambayi Ɗalibanka

Wane irin abu ne kake samarwa da ko / rabawa a intanet a halin yanzu (misali., bidiyoyi, kiɗa, waƙoki, shafukan yanar gizo, zane-zane, hotuna masu motsi)?

Me ya ba ka sha'wa har ya sanya kake raba wannan abun? Me yasa ka yi?

Wane abu ne kake da shi wanda aka danganta sunanka na ainihi da hotonka da

shi?

Shin akwai wani abun da ba ka so a danganta ka da shi a bainar jama'a? Me zai hana?

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 7 domin su tattauna. Nemi ƙungiyoyin da su raba.

**Tambayi Ɗalibanka**

Kafin mu yi magana a kan kasancewarka a intanet a nan gaba, bari mu yi magana a kan manufofinka a nan gaba. Tattauna tare da abokin hulɗarka: Ina kuma me kake so ka kasance a wasu 'yan shekaru daga yanzu a lokacin da ka girma, kuma yaya ka samar da wannan ra'ayin naka a farko? Ya yi daidai idan kana da ra'ayi fiye da guda ɗaya ko kuma wanda ya ba ka sha'awa a halin yanzu.

Wasu manufofi ne kuma kake da su da ba su da dangantaka da manufofin aikin da za ka yi a nan gaba?

Me za ka iya yi a intanet don taimaka maka wajen cimma manufarka aikin da za ka yi a nan gaba ko manufofinka na ƙashin kanka?

## Takardar darasi

**Tattaunawa a Aji**

Bayar da Takardar darasi a kan Halayyata a Intanet ga mahalarta taron.

**Sanar da Ɗalibanka**

Abun da kake yi a intanet zai iya taimaka maka wajen bincika abun da kake sha'awa a halin yanzu sannan kuma zai taimaka maka wajen gano abun da za ka yi sha'awa a gaba..

Ɗauki wasu 'yan mintuna domin ka cike wannan takardar darasin sannan ka bayyana sha'awarka a kan yanda za ka gabatar da kanka a intanet. Ka tuna cewa halayyar kowa da kowa a intanet za ta iya bambanta, kuma taka halayyar za ta iya inganta bisa ga yanda manufarka da kuma abubuwan da kake sha'awa za su canza a nan gaba.

# Aiki

## Aiki

### Sanar da Ɗalibanka

Yanzu da muka yi bayani a kan yanda za ka dubi kanka da abubuwan da kake sha'awa, bari mu yi tunani a kan yanda za ka bayar da haske a kan wani ɓangare na halayyarka ga wasu.

Kamar a ce kana ƙirƙirar wani sabon abu a dandalin sadarwar zamani wanda ya karkata ga ɓangare na halayyarka. Za ka fara tun daga farko, sannan kuma kana da damar gyara saitunan sirri gaba ɗaya da kuma samar da abu ta yanda kake so.

A cikin sakin layi, yi bayani a kan yanda za ka tsara wannan sabon abun a dandalin sadarwar zamanin don nuna hoton da ka zaɓa ga abokanka da mabiya. Musamman, yi magana a kan waɗannan abubuwa:

1. Nau'in asusu da dandalin sadarwar zamani (misali., dandalin sadarwar zamani, shafin yanar gizo, da dai sauran su).

2. Nau'in abun (misali., hotuna, bidiyoyi, aike masu ɗauke da rubutu)

3. Me za ka sanya a sashin "Game da Ni"?

4. Wasu irin hotuna za ka yi amfani da su?

5. Me za ka saita saitunan sirrinka a kai? Shin wasu daga cikin waɗannan saitunan za su dogara ne a kan nau'in abun da za ka raba?

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.